Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 016 (Pg. 176-186)

# Nazarin Wasu Ayyukan Al'adun Taimakekeniya A Bukin Auren Cike-Murhu: Tsokaci A Mahangar Direbobi Da 'Yan Kamasho Hausawa

**Nuhu Nalado**
naladonuhu@gmail.com
08067762873
School of Secondry Education Department of Hausa Studies, IKCOE D/Ma Katsina State

**Abdullahi Na'Allah**
naallah.a@unilorin.edu.ng
08038636215
Department of Linguistics and Nigerian Languages, University of Ilorin, Kwara state

**Sani Aliyu**
sanialiyu101@gmail.com
08039299012
Department of Nigerian Languages, Federal University DutsinMa, Katsina State

**Tsakure**

*Sana'ar direbanci da sana'ar kamasho suna daga cikin sana'o'in da suka shafi harkokin sufuri a rayuwar wannan lokaci da suka samo asali sakamakon hulɗa ta kai tsaye da wasu baƙin al'ummu da al'ummar Hausawa. Manufar wannan nazari ya shafi gudanar da bayanan wasu al'adun taimakekeniya da ake gudanarwa a bukin auren cike-murhu na direbobi da 'yan kamasho. Aikin ya ginu ta hanyar shiga a gudanar da al'adun a tare da masu gabatar da binciken, tare da tuntuɓar wasu mutanen da ake ganin suna da masaniya a game da al'adun. Tare da gudanar da bita daga wasu ayyukan masana da suka gabata. An ɗora wannan nazari a bisa Ra'in zumuntar sassan al'adun al'umma (Concensus theory of culture). Bugu da ƙari, binciken ya gano cewar mafi yawa daga cikin direbobi da masu gudanar da sana'ar kamasho ba su da masaniyar ƙunshiyar fassarar ayyukan al'adun da suke gudanarwa. Idan an tambaye su me hakan yake nufi za su ce, 'al'ada ce'. Daga ƙarshe, nazarin ya fahimci cewa, duk da addinin musulunci ya yi ƙarfi a zukatan Hausawa kuma suna kyautata bin umurninsa, wasu daga cikin al'ummar suna gudanar da wasu ayyukan al'adunsu da sukan kai su ga faɗawa a komar ayyukan addini gargajiyarsu. Musamman ga abin da ya shafi ayyukan neman tsari da kariya da kuma neman biyan wasu buƙatu a rayuwa.*

***Muhimman Kalmomi***: *Direbobi; 'yan kamasho; auren murhu; al'adu; taimakekeniya.*

## 1.0 Gabatarwa

Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar ɗan'Adam tun daga haihuwarsa har zuwa ƙabarinsa. Masanin ya yi fashin baƙin ma'anar a inda ya ƙara da cewa, "A ko ina mutum ya samu kansa duk wata ɗabi'a da

ya tashi da ita koya tarar ana yi tun a farkon rayuwarsa, ita ce al'ada (Bunza 2006, sh xxvii).

Wasu masana sun albarkaci al'ada da cewa, "Ita ce rumbun dukkanin tunane-tunanen da falsafa. Da ayyukan basira da dukkanin sauran ginshiƙan rayuwar ɗan'Adam" (Salim 1985, sh 1).

Al'ada aba ce maimatuƙar muhimmanci da ke saitawa tare da jagorantar rayuwar mutum ko al'uma a tafarkin rayuwa, da tsarin zamantakewa ɗungurungum (Nalado 2015, sh 3).

Al'adun gargajiya a cikin al'umma suke yin jagoranci da saita tunanin al'ummar a fagen rayuwa. Domin sun tattaro mabambanta turaku da alfanu na al'amurran rayuwa, da suka shafi fagen koyar da harshe da ilimantarwa da kuma wasu ayyukan da suke da nasaba da nishaɗantarwa (Yakasai 2012, sh 33/34).

Da wannan ne aikin ke kallon Al'ada a matsayin Sababbiyar hanyar gudanar da rayuwa. Da wani ko wasu mutane ko al'umma suka aminta da ita suke kuma ɗora rayuwarsu akai ta hanyar yin imani da ayyukan da suke aiwatarwa.

Direbobi da masu aikin kamasho suna tattare da wasu halaye da ɗabi'u, da suke a matsayin madanganta al'adunsu a rayuwa. Al'adun sun samu a sakamakon yanayin sana'ar da suke gudanarwa ta safarar kaya da jama'a a tsakanin al'ummu masu al'adu daban-daban.

Muƙalar ta ginu ne a kan nazarin wasu ayyukan al'adun taimakekeniya a bukin auren cike-murhu da direbobi Hausawa da takwarorinsu 'yan kamasho suke gudanarwa, ta fuskar samar da bayanai dangane da al'adun da kuma musabbabin aiwatar da su.

Nazarin ya gudana ne a ƙarƙashin jagorancin wasu muhimman ayyukan al'adun Hausawa da suke samuwa a gaɓar taimako daga abokanan hulɗa, a tsakanin direbobi da 'yan kamasho Hausawa. Bugu da ƙari, aikn ya samu ne ta bin ƙa'idojin da bincike na ilimi irin wannan ya tanada.

### 1.1 Sharar fage

Direbanci a Sana'o'in Hausawa al'amari ne da ya samu a sakamakon karɓar sabon tsarin sufuri da al'umma suka yi na zamani da Turawa suka samar ga al'ummun Nahiyar Africa. A inda sana'ar ta haifi sana'ar kamasho da suke gudana kafaɗa da kafaɗa da ta direbanci. Da 'yan kamashosuke gudanarwa a gurabun da ake aiwatar da ayyukan sufuri a cikin ƙasar Hausa. Tun a lokuttan da suka gabata har bisa ga wannan lokaci. Kalmar direbobi jam'in suna ne na direba da ake amfani da ita a fagen gudanar da aikin sufurin mota a ƙasar Hausa (Alfanda 2008, sh 3).

Shigar kamasho da direbanci a sana'o'in Hausawa al'amari ne mai daɗaɗɗen tarihi a tsarin zamantakewar al'ummar Hausawa. Lamarin ya faru a sakamakon wanzuwar wasu dalilai da suka haifar da kafuwar tashoshin mota a wasu manyan garuruwan Hausawa. Karɓar sabon tsarin sufuri da al'ummar Hausawa suka yi shi ne babban dalilin da ya haifar da shigar wasu mutane 'yan kasuwa da suke da tasiri a wajen yin hulɗatayyar zamani musamman da Turawa da sauran ƙabilu na cikin gida. Mutanen sun

kasance su ne suka fara yin aikin kamasho da kuma ɗaukar aikin a matsayin sana'a a cikin al'ummar Hausawa.

Alhaji Alasan Ɗantata da wani abokinsa da ake kira Alhaji Abdalla Dunu da suka rayu a garin Kano suna a matsayin sahun mutanen farko da suka fara assasa aikin kamasho a cikin al'ummar Hausawa a shekarun '1935-1955'. Hakan ya faru ne a tsakaninsu da baƙin Turawa masu sayen gyaɗa da auduga ta hanyar kamfanin *BCG* a lokacin da ya shuɗe. Sai kuma sahu na biyu da ya ƙunshi mutane irinsu Alhaji Babba Ɗankamasho na tashar Nasarawa a cikin birnin Kano, da Malam Magaji Mai'ido ɗaya da yake a garin Malumfashi ta Jahar Katsina (Sarki Labaran Kano, 2023 11/12: *You tube*).

Sana'ar kamasho tana tafiya kafaɗa da kafaɗa ne da ta direbanci ko tuƙin mota. Al'ummar Hausawa, sun shiga cikin tsarin tuƙin mota daga bisani, domin a karon farko baya ga Turawa, Yarabawa ne da wasu ƙabilu 'yan ƙasa suke tafiyar da harkar a faɗin ƙasar Hausa (Musa 2016, sh 2). Ganin alfanun tsarin Hausawa suka shiga cikin sana'ar. A farko al'ummar Yarabawa ne suka zo masu da ita kaitsaye (Ado 2015, sh 2). Waƙar Alhaji Musa Ɗangoma hujja ce ga wannan zance domin cewa ya yi:

> Jagora: Tcinananniya motar Alfa mai saurin kashe Hausawa!
> Ta ƙi Bahaushe sai Arna!
> Ko don arnan aka ƙera ki.
> (Waƙar Musa Ɗangoma. Motar Alfa: Turke na 2).

### 1.1.1 Bayanin Muhimman Kalmomin Nazari

Bayani ne da ya shafi ma'anar wasu daga cikin muhimman kalmomin da suke a cikin taken aikin. Lamarin za ya samar da ƙarin haske zuwa ga fahimtar ƙunshiyar nazarin a cikin sauƙi. Muhimman kalmomin nazarin sun kasance kamar haka:

### 1.1.2 Nazari

Kalmar nazari suna ne na namiji da yake nufin gudanar da bincike na ilimi a game da sanin wani abu ko fayyace wata matsala a rayuwa (Sa'id da wasu (editoci), 2006, sh. 358).

Gudummawar na ganin nazari a matsayin aiki na ilimi da ya shafi bijiro da wasu keɓaɓɓun bayanai a kan wani batu da nufin inganta rayuwa da ciyar da ilimi gaba.

### 1.1.3 Taimakekeniya

Kalmar taimako ce da ta ke ɗauke da suna na namiji a harshen Hausa. Ma'anar na nufin agaji ko gudummawa (Sa'id da wasu (editoci), 2006, sh. 420). A inda gudummawar ke ganin al'amari ne da ya shafi taimaka wa juna a yayin tafiyar da rayuwar wani ko wasu a tsarin zamantakewa ta yau da kullum.

### 1.1.3 Direba

Kalmar "direba" suna ne da ake amfani da shi a fagen gudanar da aikin sufurin mota a ƙasar Hausa. Tana ɗaukar kalmar direbobi a sigar jam'i. Al'amari ne da ya samu assasuwa tun daga bayyanar sababbin hanyoyin gudanar da sufuri a tsarin rayuwa da zamantakewar Hausawa (Alfanda 2008,

sh. 3; Musa 2016, sh. 2). Kalmar madugu wadda ake yiwa laƙabi da uban tafiya ko jagaba ta kasance a matsayin kwatankwacin sunan kalmar direba ta asali a tunanin Hausawa. Sakamakon madugune yake shugabantar ayari da matafiya daga wani gari zuwa wani gari ta yin amfani da dabbobi ko kuma tafiya a ƙasa, (Imam, 1933, sh 291, da Bambali, 2007, sh 47).

### 1.1.4 Ɗankamasho

Kalmar Ɗan Kamasho ta samu ne daga kalmar kamasho, wadda ta ke nufin suna na mutum a jinsin namiji kuma tilo. Ta fuskar ilimi kuwa, lamarin na kasancewa ta fuskoki guda uku (3) mabambanta.

1. Kuɗin la'ada da ladan da ake ba mutum yayin da ya samo wa wani kasuwa, musamman wanda direbobi kan bayar.
2. Sunan mutumin da yake zaune a tasha yana samo wa direbobi fasinja a ba shi lada.
3. Ana kiran sana'ar kaco-am da wannan suna na 'yan kamasho a cikin sigar jam'i (Sa'id da wasu 2006, sh. 228).

Nazarin na ganin kalmar na samun wakilcin 'yan kamasho a cikin sigar jam'i. Ta fuskar ma'ana kuma sun kasance wasu mutane ne masu hukuncin zartar da harkokin sufuri na zamani a ciki da wajen tashoshin mota da sauran cibiyoyin gudanar da sufuri a tsakanin al'umma a wannan lokaci.

Ma'anar kalmar a gargajiyance ko sunan aikin a gargajiyar Hausawa shi ne zangomako fatomi. Kasancewarsa aikinsa ya shafi kula da matafiya da ɗaukacin kayansu ga al'amarin da ya shafi sufuri daga gari zuwa gari, (Alhassan 1988, sh. 54; Love Joy 1980, sh. 102).

### 1.1.5 Al'ada

Al'ada na a matsayin wata sababbiyar hanyar tafiyar da rayuwar al'umma da suka yi Imani da ita kuma suna ɗora rayuwarsu a kai. Al'adu sun kasance jam'in suna ne na kalmar al'ada a rayuwar Hausawa (Nalado 2017, sh. 55).

## 2.0 Manufar Bincike

Manufar binciken ita ce a gudanar da bayani ta hanyar fashin baƙin ayyukan al'adun Hausawa da ake gudanarwa na taimakeniya a gurbin auren cike-murhu da direbobi da 'yan kamasho Hausawa suke gudanarwa a lokacin da suke aiwatar da bukin auren cike-murhu.

Wata manufar gudanar da wannan bincike ta shafi sanin ma'anar auren cike murhu da sanin yanaye-yanayen al'adun da mutanen suke gudanarwa a yayin aiwatar da wannan yinin buki, da matsalolin da al'adar take fuskanta a wannan lokaci domin samun damar ilimantar da al'umma da ciyar da turbar ilimin al'adun Hausawa gaba.

### 2.1 Ra'in Bincike

An ɗora nazarin a bisa Ra'in haɗin kan sassan al'umma, watau ra'in zumuntar sassan ayyukan al'umma *(Consensus theory of culture)*. Emile Durkheim ne ya kasance mutumin da ya assasa Ra'in a shekarun 1792 zuwa1793. Daga cikin magoya bayan Ra'in akwai Auguste Comte (1898 – 1957). Dangane da cikin gida kuwa, akwai magoya bayan Ra'in da suka haɗa da Ado, (2025, sh.

22; Nalado 2025, sh. 3). Manufar ra'in zumuntar sassan al'umma ita ce, tabbatar da samun jituwa da ɗorewar zaman lafiya da taimakon juna cikin walwala a tsakanin mutane ko al'umma, domin su rayu a matsayin tsintsiya ɗaya, ta fuskar samar da haɗin kai da taimakon juna a tsakaninsu.

Dangantakar ra'in da aikin a bayyane yake, idan aka yi duba da manufarsa da kuma taken wannan bincike da aka gudanar. Duba da cewar bincike ne da ya shafi wasu ayyukan al'adun al'ummar Hausawa a bukin auren cike-murhu da direbobi Hausawa da takwarorinsu 'yan kamasho suke gudanarwa. Shi kuma ra'in, yana magana ne a kan ayyukan zumuntar sassan al'umma a rayuwa. Ra'in yana kallon al'umma a matsayin wadda take da sassa daban-daban waɗanda suke gudanar da zamantakewa a tare ta hanyar taimakon juna.

## 3.0 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Ta fuskar tsarin gudanarwa, bincike ne irin na bayyanawa da ya shafi gabatar da fashin baƙin ƙunshiyar wasu ayyukan al'adun taimakekeniyar direbobi da 'yan kamasho Hausawa a gurbin bukin auren murhu. Nazarin ya ginu ta hanyar lura da yadda ake gudanar da al'adun a yayin bukin, da kuma shiga a gudanar da al'adun a tare da masu gabatar da binciken. Tuntuɓar wasu mutanen da ake ganin suna da masaniya a game da al'adun da kuma gudanar da bita daga wasu ayyukan masana da suka gabata suna daga cikin hanyoyin da binciken ya samu ginuwa.

Bugu da ƙari, an yi amfani da dabarar zaɓin ganin dama, a gurbin zaɓen nau'in al'adar da aka yi nazari a game da ita. A inda aka zaɓi al'aladar da ake kyautata zaton za a iya samun sahihan bayanan da ake buƙata. Aikin ya shafi wasu yankuna na ƙasar Katsina da Maraɗi da take a cikin Jamhuriyar Nijar.

## 3.2 Aure a Rayuwar Direbobi da 'Yan Kamasho Hausawa

Kamar sauran mutane da suke rayuwa a cikin al'ummar Hausawa, direbobi da takwarorinsu 'yan kamasho suna gudanar da al'amurran da suka shafi aure a rayuwarsu ta yau da kullum. Yanayin muhallin da waɗannan mutane suke gudanar da al'amurransu da kuma yanayin ƙarfin tattalin arziƙi ta fuskar samayyarsu, ya taimaka a wajen yin riƙo tare gudanar da aure ta fuskoki mabambanta. A inda auren ya ƙunshi nau'oin aure guda biyar da suka haɗa da: Auren fari da auren garari da auren murhu da auren rufe ƙofa da auren gadara. A inda auren kome yakan kasance daga cikin rukunan auren da mutanen suke aiwatarwa face a gurbin auren fari.

## 4.0 Auren Murhu

Auren cike-murhu, al'ada ce da take nufin mutum ya yi ƙarin aure daga mata biyu zuwa mata uku. Auren ya samu sunansa ne daga sigar duwatsun murhu guda uku, da ake amfani dasu a gidan kowane Bahaushe a rayuwar gargajiya (Ɗanbala Manu, *7/8/24*. Hira: Tsohon direba a garin Dutsi Jihar Katsina).

## 4.1 Taimakekeniyar Direbobi da 'Yan kamasho a Gurbin Auren Cike-Murhu

Al'adun taimako ne da suka ginu a gurbin aure na yau da kullum da wasu direbobi da 'yankamasho Hausawa suke aiwatarwa a

rayuwasu. Taimakekeniyar ta ƙunshi na tsarawa da shirya zaman, tare da bayar da tallafin kuɗaɗe da suturu da wasu magungunan kyautata zamantakewar iyali a yayin zaman aure.

A irin wannan yanayi, abokanan hulɗar direbobi da 'yan kamasho suna shirya wasu ayyukan gudummawa na musamman ga abokinsu da ya yi auren. Musamman idan ya kasance a yayin auren ya haɗa mata guda biyu masu sunaye iri ɗaya. Wato ya kasance ya zamanto mai asin da asin ta fuskar sunayen matansa na aure.

A irin wannan hali, nazarin ya fahimci idan matar da ya aura ta biyu a gurbin auren garari sunanta ya zamanto iri ɗaya da sunan matar da ya cike-murhu da ita, mijin da abokanansa sukan shirya wani ƙwarya-ƙwaryan zama na yini ɗaya a ƙofar gidansa.

A yayin zaman, za a sami sababbin tabarmi farare na karauni (kaba) guda uku ko bakwai a zauna a samansu. Shi kuma angon za ya sanya farar riga 'yarshara sabuwa da wandonta da kuma takalmin fata da farar hula ta haɓar kada. A inda za ya zauna a tsakiyar abokansa su ci gaba da barkwanci da hira. A lokacin da ake gudanar da hirar, uwar gidan direban ko ɗankamashon da ya yi auren, za ta aiko masu da goruna uku. Kowane gora yana cike da nau'in abu daban.

Gora na farko yana cike da ruwa. Gora na biyu na cike da maɗi ko zuma, gora na uku kuma na cike da madara. Gorunan kuma za su kasance na duma ne.

A wannan gaɓa ce, abokansa za su umurce shi da ya fara ɗaukar goran da ya ke so amma idanunsa za su kasance a rufe. Gora na farko da za ya ɗauko yana wakiltar uwar gidansa. Duba da sigar abin da ke a cikin goran ne abokanansa za su yi fashin baƙin zamantakewarsa da iyalinsa da kuma cikarsa gogaggen namiji.

Idan a karon farko ya ɗauko goran ruwa, abokanansa da sauran mutane za su ba shi gudummawar yaji dakan maza wanda a bisa ga al'ada za su zo da wannan yaji a muhallin da ake gudanar da zaman. A yayin da ya ɗauko zumuwa ko maɗi maroƙi za ya sanar da mutane ta hanyar yin he. A wannan gaɓa, matan da suke a cikin gida za su yi guɗa har sau uku. Hakan yana nuna cewar matan da aka tarar suna da jituwa da mijinsu ta fuskar zaman aure.

A yayin da angon ya ɗauko goran madara a karon farko, abokanansa da sauran mutane na cikin gida za su ce a shiga ɗaki lafiya. Daga ƙarshe abokanansa za su miƙa masa wani abu a fagen gudummawar biki. Daga nan kowa za ya kama gabansa (Rabe Bega Direba 10/5/23. Hira: Tsahar motar garin Kankiya Jihar Katsina).

### 4.1 Fashin Baƙin Wasu Muhimman Ayyukan Al'adun Hausawa a Bukin Auren Cike-Murhu

Nazarin ya gabatar da sharhi ko fashin baƙin ƙunshiyar wasu muhimman al'adun Hausawa da ake gudanarwa a gaɓar wannan yinin buki na auren murhu a rayuwar direbobi da 'yan kamasho Hausawa. Musamman ga mutumin da ya yi dace ta hanyar haɗa matan aure guda biyu masu sunaye iri ɗaya (Asin da asin).

#### 4.1.1 Amfani da Fararen Tabarmin Kaba Maaraa

Amfani da tabarmin kaba mara guda uku ko guda biyar ko guda bakwai, da ake samu daga cikin taimakekeniyar da ke gudana a tsakanin abokanan hulɗa a yayin gudanar da wannan al'ada ya kasance muhimmin al'amari a yayin gudanar da bukin. Nazarin ya fahimci cewa, an keɓanta ga yin amfani da fararen tabarmi ne na karauni ba tabarmar malfa ko wundi ba. Ganin al'amari ne da ya shafi harkar aure da ake buƙatar ya yi albarka da kuma samun ɗorewar zaman lafiya. Kasancewar a gargajiyance, al'ummar Hausawa suna da imanin cewa a duk wata harkar da ta shafi hidimar gudanar da aure, matsara na wannan gida suna halartar wurin da ake yin duk wata hidima da ta shafi bukin ko da kuwa ba a gayyace su ba. Idan sun zo a wajen suna buƙatar farar tabarma da ba a yi wa turi ko ratsin wani launi ba. Samun halartarsu a yayin da ake gudanar da zaman abun alhairi ne ga rayuwar auren (Ali Tarno Kukarƙwaida, Hira: A wajen bukin cike-murhu a garin Shibdawa, 12/4/24. Karamar hukumar Bindawa ta Jihar Katsina).

Nazarin ya fahimci ɗabi'antuwa da al'ummar ta yi wajen yin amfani da nau'in waɗannan tabarmi a yayin gudanar da hidimar da ta shafi ƙaruwar aure da haihuwa ya haifar da tsarin ya zamanto al'ada. Duk da cewar wasu daga cikin masu amfani da tabarmin a wannan gaɓa, basu da masaniyar hakan. Wannan dalili ne ya haifar da a kusan kowane ƙauye da ke a ƙasar Hausa a yau, idan za a gudanar da hidimar raɗin suna ko ɗaurin aure ake yin amfani da farar leda da ake samu daga fararen buhuna a ɗinke su, su zama shimfiɗa a sakamakon ƙarancin tabarmin kaba (karauni). Ma'ana suna yin kwaikwayo ta sigar kamanceceniya.

Idan kuma zama ne da ya shafi zaman makoki ko zama na jaje, a wannan gaɓa ana yin amfani da sauran tabarmi da shimfiɗu masu launi daban-daban, na zamani da kuma na gargajiya (Amadi Dattijo 'Yandoma, 18/3/24. Hira: A wajen da yake saƙa tabarmi a cikin gonarsa).

Nazarin yana ganin yin amfani da tabarmi akasin farare yana faruwa ne a sakamakon abin da ya assasa zaman bana farin ciki ko ƙaruwa ba ne.

#### 4.1.2 Amfani da Farar Sutura

Aikin ya fahimci suturar da ake taimaka wa mutumin da ya yi auren a wannan gaɓa, ta ƙunshi farar riga 'yarshara sabuwa da wandonta da kuma takalmin fata. Sai farar hula ta haɓar kada, a inda mutumin da ya yi auren za ya sanya kayan ya zauna a tsakiyar taro.

Zama a bisa dutsen murhu ga magidanci Bahaushe da kuma yin duk wata ɗabi'a mai nasaba da murhu (Ukuntawa), ɗabi'a ce ta aljani Nakada a tunananin gargajiyar Hausawa. Riga 'yarshara fara da hula haɓar kada kuwa, dukkaninsu kayansa ne (Zulai 'Yarbori, 16/10/24: Hira a ƙauyen Kartaka a bukin 'yan bori, a ƙaramar Hukumar Charanci).

A gefe guda, suturun sun kasance farare sakamakon Hausawa suna danganta duk wani abu fari da cewar al'amari ne mai tattare da haske ko albarka, ko abu ne mai nasaba da addinin musulunci. Misali fararen Aljanu ana masu kallon musulman aljannu

kuma aljanu masu kirki ta fuskar ɗabi'a. Bugu da ƙari, farar sutura ta aljani Malam Alhaji ce. Shi kuma malam Alhaji aminin aljani Nakada ne (Zulai 'Yarbori, 16/10/24: Hira a ƙauyen Kartaka a bukin 'yan bori, a ƙaramar Hukumar Charanci). Nazarin na ganin neman dace da tubarraki ta sigar kwaikwayo ya taimaka wajen faruwa da kuma gudanar da ɗabi'ar a yayin gudanar da bukin auren cike-murhu ga direbobi da takwarorinsu Hausawa a wannan lokaci.

### 4.1.3 Fashin Baƙin Goruna uku da Kunshiyarsu

Nazarin ya yi bayanin cewa a lokacin da ake gudanar da hira, uwar gidan mutumin da ya yi auren za ta aiko masa da goruna uku da ake samu daga cikin gudummawar da wani abokin hulɗarsa direba ko mai kakamasho. Kowane gora na cike da nau'in abu daban.

Gora na farko yana ɗauke da ruwa. Gora na biyu yana ɗauke da maɗi ko zuma gora na uku kuma yana ɗauke da madara. Gorunan kuma za su kasance na duma ne. Abokansa za su umurce shi da ya fara ɗaukar goran da ya ke so amma idanunsa za su kasance a rufe. Gora na farko da za ya ɗauko yana wakiltar uwar gidansa. Duba da sigar abin da yake a cikin garan ne abokanansa za su yi fashin baƙin zamantakewarsa da iyalinsa da kuma cikarsa gogaggen namiji.

Bayanai sun gabata cewar idan a karon farko ya ɗauko goran ruwa, abokanansa da sauran mutane za su ba shi gudummawar yaji dakan maza wanda bisa ga al'ada za su zo da wannnan yaji.

Idan kuma ya ɗauko zumuwa ko maɗi matan da ke a cikin gida za su yi guɗa har sau uku. Hakan yana nuna cewar matan da aka tarar suna da jituwa da mijinsu ta fuskar zaman aure.

Aikin na ganin an yi amfani da gorunan duma ne da abubuwan da suka ƙunsa a sakamakon kwaikwayon fata a gurbin ɗabi'a ko halayyar wani abu a rayuwa (Sallau 2015, sh 5).

A gargajiyance, al'ummar Hausawa na yiwa ƙwarya ko duk wani ɗan duma kallon wani abu mai tattare da al'barka. A inda suke da tunanin idan aka yi amfani da ƙwarya ko ɗiyan duma a wani al'amari za a samu cin nasara da kuma yaɗuwa. Nazarin na ganin wannan dalili ne ya haifar da zaɓen gorunan duma maimakon tulunan ƙasa. Haka zalika, aikin na ganin wannan dalili ne ya sa ake yin amfani da masaki a yayin gudanar da wankan jego a lokaci haihuwa a gargajiyance.

### 4.1.4 Al'adar Shiga Ɗaki Lafiya

Nazarin ya kawo bayanan da ke yin nuni da cewa, a yayin da angon ya ɗauko goran madara a karon farko, abokanansa da sauran mutane na cikin gida za su ce, "A shiga ɗaki lafiya".

Masana ayyukan da suka shafi al'adun Hausawa sun ayyana cewa, "Kallon yanayi da halayyar faruwar wasu al'amura a muhallan da Ɗan'adam yake rayuwa na a matsayin mizanin farko na samuwar wasu ayyukan al'adun al'umma a gaɓar kwaikwayo ta fuskar ɗabi'a (Sallau 2015, sh 5). Hakan ya sa gudummawar nan ta yi itifaƙin cewa, mutanen sun yi amfani da

ɗabi'a da halayyar madara suka danganta lamarin da haihuwa. Domin madara albarka ce ta abin sha da ta ke samuwa a sakamakon shayarwa a gurbin haihuwa. A yayin shiga ɗaki a karon farko, angon ba za ya kutsa kai cikin ɗakin gaba ɗaya ba. Za ya dafa bangon ƙofar ɗakin amaryar ya ce,

> Gafaranku dai, ga mu nan shigowa!
>
> 'Ya'yan malga da bagaruwa su rufo baya.

Bayan ya faɗi waɗancan lafuzza sai ya zura ƙafarsa ta dama a cikin ɗakin ya fiddo ta waje har sau uku da sauri. A cikon na ukun sai ya shiga ɗakin. Idan ya shiga a karon farko za ya dumtsi aya da za ya tarar ya ci. Ya kuma zauna a bisa sabuwar tabarmar kaba fara ta karauni. (Rabe Bega Direba, 10/5/23. Hira: Tsahar motar Kankiya ta Jihar Katsina).

Nazarin ya fahimci angon yana yi wa matsaran gidan da aka yi imani da wanzuwarsu a gargajiyance sallama. Waɗanda ake kyautata zaton suna zaune a saman wannan sabuwar tabarma. Zura ƙafa sau uku wata alama ce da ta shafi addinin gargajiyar Hausawa da ke yin nuni da cewar su matsaran za su san da shigowar angon a ɗakin a karon farko. Idan matar (amarya), ta shigo da wata manufa ko baƙar tambaya yin hakan na a matsayin karya waccan matsala (Malam Sani Diilai, 13/3/23. Hira a ƙauyen Tudun Alhaji, ƙaramar hukumar Tsafe ta Jihar Zamfara).

Ambato 'ya'yan malga da bagaruwa kuwa, ya ta'allaƙa ne a gurbin fatar samun haihuwa da matar da aka aura. Kasancewar itatuwan da aka ambaci sunayensu itatuwa ne da suke haihuwar 'ya'ya da yawa a lokaci guda, kuma 'ya'yan suna bin jikin itatuwan. Hakan ne yasa ake fatar yaran da za a Haifa su yi yawa da biyayya ga maifansu (Malam Sani Diilai, 13/3/23. Hira a ƙauyen Tudun Alhaji, ƙaramar hukumar Tsafe ta Jihar Zamfara).

## 5.0 Sakamakon Bincike

Nazarin yana ganin direba ko mai kamasho ya cike-murhu, ko ya yi murhu ta fuskar aure abin ƙima da alfahari ne a rayuwarsa, da kuma a tsarin zamantakewarsu tun a lokuttan da suka gabata har bisa ga wannan lokaci.

An fahimci yanayin tattalin arƙi ta fuskar samayya dake a tattare da direbobi Hausawa da masu aikin kamasho ya kasance dalilan ci gaba da yin riƙi tare da gudanar da ayyukan wannanan al'ada, da kuma kyautata ta a rayuwarsu. Haka zalika, wannan dalili ne ya haifar da danganta gudanar da ayyukan al'adar ga waɗannan mutane. Ganin cewa al'amari ne na samar da annashuwa da ke buƙatar kashe kuɗaɗe.

Bugu da ƙari, nazarin ya gano cewar mafi yawa daga cikin direbobi da masu gudanar da sana'ar kamasho da suke gudanar da waɗannan al'adu ba su da masaniyar ƙunshiyar fassarar ayyukan al'adun da suke gudanarwa. Idan an tambaye su me hakan ya ke nufi za su ce, 'al'ada ce'.

Daga ƙarshe, nazarin ya fahimci addinin musulunci da ya yi ƙarfi a zukatan Hausawa kuma suna kyautata bin umurninsa, bai kange wasu daga cikin al'ummar Hausawa ga barin wasu ayyukan addini gargajiya ba. Musamman ga abin da ya shafi ayyukan

tsari da kariya da neman biyan buƙatu na rayuwa ba. Haka kuma, a yau wasu daga cikin direbobi da takwarorinsu masu sana'ar kamasho, suna aiwatar da taimakekeniya a gaɓar tafiyar da rayuwarsu, musamman a bukin auren murhu da nazarin ya ginu a kai. Duk da cewar gudanar da ayyukan al'adar suna raguwa da kaso mai rinjaye a tsakanin direbobi da 'yankamasho Hausawa a wannan lokaci a sanadiyyar matsalolin tattalin arziƙi.

### 5.1 Shawarwari

Kasancewar kowane mutum, ko al'umma na rayuwa ne a matsayin wakili ko jakadan al'adun gargajiyarsa. Mutuƙar dai ya kasance mutumin ko al'ummar suna yin amfani da harshensu na uwa da sauran al'adun gudanar da zamantakewa. Zai kyautu, idan ɗaliban ilimi suka himmantu wajen zaƙulo mabambanta ayyukan al'adun Hausawa da ake aiwatarwa a muhallai daban-daban domin samun damar taskace al'adun da ƙara kyautata su ta fuskar ilimi.

### 5.2 Kammalawa

A wannan gaɓa ce nazarin ya samu kammaluwa sakamakon halarto da jawaban da suka gabata a ƙunshiyar aikin. A inda bayanan suka mayar da hankali a game da fashin baƙin ƙunshiyar ayyukan taimakekeniyar direbobi da 'yan kamasho a bukin auren murhu da wasu daga cikinsu suke aiwatarwa a ƙasar Hausa a wannan lokaci. Nazarin ya gudana ne a kan fashin baƙin ƙunshiyar wasu ayyukan al'adun taimakekeniyar direbobi da 'yan kamasho Hausawa a bukin auren murhu. An yi ƙoƙarin yin fashin baƙin ƙunshiyar taimakekeniyar da mutanen da aikin ya ginu a kansu suke bayarwa a gurabun yin amfani da fararen tabarmi karauni mara. Da yin amfani da farar sutura ga ango tare da yin fashin baƙin ƙunshiyar goruna guda uku da waɗanda abin ya shafa suke taimakawa da su a yayin gudanar da wannan al'ada. Fashin baƙin muhimmiyar al'adar nan ta shiga ɗaki lafiya dangane da yadda direba ko maikamasho suke aiwatar da ita a wannan gaɓa, na daga cikin abin da ya shafi aikin. Daga ƙarshe an halarto da bayanan sakamakon bincike da shawarwarin da suka shafi binciken a wannan fage a al'adun taimakekeniyar direbobi da 'yan kamasho Hausawa a bukin auren cike-murhu.

## MANAZARTA


Alfanda, A. A. (2008). "Rubuce-rubuce a jikin motocin sufuri a birnin Kano da kewaye: manufarsu da matsayinsu ga al'umma'. Kundin Digiri na Farko. Jami'ar Bayero.

Ado, A. (2025). Falsafar ra'i da karin magana a faifan nazarin ɗora al'adun Hausawa kan ra'oin bincike. Kundin Laccar Ɗalibai masu Nazari a kan Ra'o'in Al'adun Hausawa. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Ado, A. (2021). *Dabarun gudanar da bincike na ilimi a kan Hausa.* Government printing Department.

Ado, A. (2017). *Ra'o'in bincike kan al'adun Hausawa.* Kanki Classical Media Enterprises.

Alhassan, H. da Musa, I. da Zarruƙ, M. R. (1988). *Zaman Hausawa.* Islamic publcations Bereu.

Bambali, N. (2007). *Komin nisan dare.* Amana Printing Press.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Tiwal. Nigeria Limited.

Bunza, A. M. (2000). "Kurkura da matakan la'anta a rayuwar Hausawa". Lakcar

da aka gabatar a ɗaliban aji huɗu masu nazarin B.A Hausa, Sokoto: Sashen Koyar da Harsunan Najeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Bunza, A. M. (2013). Hutawa ka alewa, mangyaɗa ka tuyar ƙosai: Barazanar yanayi da lokaci a kan al'adun Hausawa. Takardar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani na ƙasa da ƙasa a kan taɓarɓarewae al'adun Hausawa. Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Frank, Edward. (1987). *Culture and society.* Londo: Edimberg Press.

Imam, A. (1933). *Magana jari ce littafi na uku.* Northern Nigeria Publishing Company.

Love Joy, P. E. (1980) *The caravan of kola: The Hausa kola trade 1700-1900.* University Press Limited.

Musa, D. A. (2016). Al'adun Hausawa a cikin karin magana. Kundin Digiri Na Farko. Kano: Jami'ar Bayero.Tafawa Ɓalewa, A. (1966). *Shehu Umar.* Northern Nigeria Publishing Company limited.

Nalado, N. (2017). "Dangantakar camfin Bahaushe da kimiyar zamani". Kundin digiri na biyu.
Sashen Nazarin Harsunan Nageriya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Sa'id, B. etel (2006) *Kamusun Hausa.* Jami'ar Bayero.

# Larabci (Arabic)